TAWA TASAMENI
__________ NA HALIMA ABDULLAHI K/MASHI________
Tindaga nan bansan inda kaina yake ba sai a Rimi Clinic lokacin ma bayan magriba ne na farfado,Dakin dam da mutane, Babana shine kusa dani yana rike da hannuna,ina farfadowa shina soma gani na shiga 'yan dube dube ina kokarin tuno me ya faru?Babana ya dubeni sannu uwata ya jikin?duk yan dakin kowa ya shiga yi min sannu,hannuna na daga zan share fuskata sai naga lalle sai na tuna ashe fa ni Amarya ce nan take na tuna mai ya faru da sauri na tashi zaune nace Babana kaji abinda Adams yayi min ko?yace ya fasa aurena, babana ya rungume ni kiyi hakuri kar ki damu,sai a sannan na dubi mutanen dakin Alhajine da yaya Kabir da yayanmu sai Mama da Aunty Yagana nace ashe har su yayanmu sun iso dako Adams yace min tare zasu zo sai kuka ya kwace min babana da Alhj sai lallashina suke mama kam cewa tayi saiki yi tayi tunda yace bai sonki dole ne?cikin kuka nace mama yace har yanzu fa yana sona saidai ba zai aureni ba kila ma yana tsokanata ne,na dubi yaynmu nace dan Allah yayanmu tare kuka zo?harara ya sakar min sannan yace kiyi wa mutane shiru ynxu da kike magana gobe ne daurin aurenshi a yola can garinsu kuma iyayenshi sun. bada hakuri dan da yarinyar suka so ya aura yaki tashi daya yace yanajin inbai auri yarinyar ba mutuwa zai yi ina ganin shima ba laifinshi bane da akwai wani abu,mama tace ba komai Abdulrahim wulakancin shine kawai dan cin mutunci sai da ya bari ana saura kwana uku biki sannan zai ce ya fasa ga shi mun gayyaci mutane ya zamuyi kenan?ai gsky abinda Adamu yayi mana sai dai muce Allah ya saka mana,Babana yace ku dai ku yi hakuri ynxu mu samu kanta in yaso sai mu san abin yi,da sauri nace yawwa Babana don Allah ku taimaka min ku shawo kan Adams ina sonshi, Mama ta kawo min duka Alhj ya tare har suna hada baki shida babana suna cewa Habiba haba menenebna duka?shi ko yaynmu fita yayi, jim kadan sai ga su Doctor yace ciwona bai tashi ba na dai firgita shi yasa amma a guji tashin hankali dan haka ynxu ya sallameni,mun fito kan titi gurin da suka ajiye motoci Alhj yace na shiga motar nace ni ba zani can gidan ba baba yace to muje nan ma nace a'ah,mama haushi ya

kamata tace to ko gidansu Adamun zakije?sai kin dawo nace ni Anty Yagana zan bi Alhj yace to kuje,ya dubi yayanmu yace kai su Abdulrahman,a mota ina jikin Anty Yagana a kwance shi kuma yana tuki Anty tace Abdulrahim yaya abokinka yayi mana haka?yace anty ni kaina na rasa gane kan abin jiya fa muna tare da shi bayan mun tashi daga wani wasa wanda dama ranar zamu gama yau mu taho gaba daya da abokanmu dan har na ma Kabir waya akan ya kama mana Hotel zamu sauki baki a jiyan da daddare sai ga shi wai shi Ghana yake son zuwa ya je yaga Aisha,nace wacece kuma Aisha?sai yace yarinyar nan da aka ce ya aura yaki yanzu kuma ita yake so,da kyar ya kai safe, yau da sassafe ya dau hanya babanshi ya min waya wai ko da wata matsala ne tsakaninshi da Iman?nace ba komai shine babanshi yace to ynxu yace yau ya ke son ya auri Aisha ba sai gari ya waye ba koda suka ce a'ah su ba zasu yi karanta ba sai ganinshi sukayi ya fadi sumamme shine fa ba shiri suka dau hanyar Yola,Babanshi din yace in sun dawo zasu zo nan su bada hakuri.Jin wannan Ibr sai wani sabon kuka na saki dan lokacin sai naji wani son Adams din ma nakeyi,yaynmu ya daka min tsawa yi mana shiru ko na tsaya na bubbuge ki, wannan bakin ya yi tsit nayi shiru har mukaje gidan anty yagana.

Washe gari ina kwance anty yagana ta shigo ta dubeni tashi Iman kiyi wanka ko kya ji dan dadi nace dan Allah anty ya zanyi wannan lallen ya fita ne?na tsaneshi tace ba zai fita ba sannan ke da kike Amarya ya za'ayi ki goge lalle da sauri na tashi Adams din ya dawo yace zai aureni ne?Anty tace ni dai ban sani ba Babanki da Alhj sun ce a ci gaba da shirye shirye biki ba fashi sai dai ina zaton ba da Adams din ba ne nan na koma na kwanta na dora sabon kuka nace TAWA TA SAMENI ni iman aure ban san mijina ba?na shiga uku,Aunty yagana tayi ta bami hakuri gami da lallashi.. Ashe abinda ke faruwa shine boka yayi aiki sun hada Adams da aljani ya juyar mishi hankali dan haka da suka samu Ibr zancen aure ya rushe da Adams sai murna da farin ciki hatta Aunty Mimi tayi murna dan dama tace bata son in auri Adams dan kar mu zama abokai,a cewarta in auri abokin mijinta taci baya(hahhhah lallai a gaisheki mimi)ita tana auran mai kudi nima na auri mai kudi ba

zai yiwu ba..Zaune gaban boka Haj Yaya ce da Haj Laure suna murna gami da godiya boka ya katse su to ynxu kunsan wanda za ta aura ko?Haj yaya tayi sauri tace duk ma wanda zata aura Allah gafarta boka taje ta tayi ta aura tunda dai ta rabu da abokin dana ai shi kenan dama bani son ta rabu dana kusa da dan nawa ne bare shi kansa,ta cigaba dan haka tun da duk kanmu....Haj Laura ta karasa da cewa ya fada kan kowa,sun bashi kudi da alkawarin in wata matsala ta taso zai gansu.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Yaune juma'a kuma yaune lunchn,nace ma anty yagana nifa ban san wanene mijin ba anty yagana tace inje don kada mutane su gane halin da ake ciki tun da ba kowa ne ya sani ba ki kwantar da hankalinki Babanki yaba Alhj damar ya fidda miki miji a cikin kwana ukun da suka rage shi kuma ya fitar miki da miji dan gaske ki dauka haka Allah ya tsara,cikin kuka nace Aunty wanene?tace nima ban sani ba dan ko mamanki bata san kowa ye ba sai dai tace tasan ba zai miki mugun zabe ba shi yasa ma kikaji nace dan gaske.Ina ji ina gani ta shirya ni suka zuba min dubai less da gwala gwalai nace anty ni dai kayan Adams ne ku cire min,tace a'a ba nashi bane ai ke yar gata ce wannan cikin kayan da babankk ya hado maki ne daga dubai sannan mamanki da Alhj sun maki gwala gwalai shima Adams ya bar maki akwatuna,dan haka in kinje gidan ango sai kiyi ta kwaliya,na share hawayen idona,Anty Saudatu ta miko min kayan shafa nan na kuma yin wata kwaliyar.

Gurin lunchn yayi guri ko ina ya tsaru mutane kamar kasa har abin ya bani mamaki ni da kawayena muka hau high table shalele ya cashe sosai su Mami da Amira da sauram kawayena sun yi min kara wajen buga abubuwa,na sha liki gurin dangi da yan uwa sun min liki baran ma Kabir har nace a raina kodai da Kabir din aka hadani ne?yaynmu ne ya bani mamaki ko leke duk yanda muke dashi shine ko yazo bikina niko a na shi

nayi rawa nayi tsaki ba komai duniya ce.Bakwai aka tashi daga gurin lunchn, gidansu Anty Yagana muka koma kuma can aka min kamu sai dai banga dangin miji ba kamar yanda naga ana yi a al'ada
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Washe gari daurin aure tun safe direban babana yaxo ya daukeni ya maidani gidan Babana nan na samu gidan cike da yan garinmu har da tsohuwa jikinta na fda na soma kuka tace kuji mun sakarai ai ni murna nayi da dan Ball yace baya yi dan Allah ya sani tunda akace Adamu Ball yake sai naji bana sonshi ynxu da babnki ya mana bayani yace ya fasa nace gara haka kila ma yace ba zai iya rike ki bane yace ba yayi tunda Ball ai ba sana'a bace, duk da halin da nake ciki sai da na yi murmushi a raina nace to shi wannan baki san ta sana'ar ba kila ma gara Ball.Karfe biyu gidan babana ya soma cika da yan daurin aure niko ina can dakin Babana na kudundune sai kyarma sanyi nake zazzabi ya rufe ni ba wanda ya san inda nake ban sani ba har an daura aure su Amira sunzo muje gurin sai nemana ake gidan cike yake dam da jama'a can babana ya shigo bedroom dinsa yana cewa bari ya karoma baki dabino sai ya sameni kwance ina ta rawar sanyi da sauri ya iso gurina,uwata menene?dama kina nan?ya dago ni jikina zafi rau ya shigo falo ya shiga kiran Anty Maijidda a waya data zo yace mata gani nan ba Ify shi kuma ya fita ya sallami baki ya dawo,Anty Maijidda ta dagani ta zaunar dani ta dubi babana tace to baban Iman ya za'ayi ynxu?ga gidan dinke da mutane ko zaka kira likitan mu ne?yace a'a bari na kira wata likitar kin san tana da matsalar zuciya ya dubeni kin san number Doc dinki na girgiza kai alamar a'a yace to bari na kira yaynku ai shi yana da no dinsa ko?nayi alamar eh,ya shiga neman layin yaynmu Anty Yagana ta yowa Anty Maijidda waya wai inzo yan walima sun soma zuwa Anty Maijidda tace yagana ga Iman nan kwance babu Ify ynzu ma likita muke kira,Anty Yagana tayi salati tace gamu nan zuwa babana ya samu yayanmu ya

sanar dashi yazo da likita gani nan ba Ify yayanmu cikin rikicewa yace ba dai ciwon ta bane ko,babana yace shi yasa nace kazo da liktan ta dan kar abin yayi nisa,jim kadan sai ga yayanmu shida likita daga dakin babana aka daukoni zuwa falo kan doguwar kujera aka kwantar dani likita ya shiga dubani can ya dago ya dubi su babana da yaynmu yace ba ciwon ta bane damuwa ce ta saukar da zazzabin sai dai ayi kokarin ganin ta rage damuwar dan tana iya kawo barazana ga ciwon nawa,ya rubuta magunguna yace zaije da kansa ya siyo sannan yace da yaynmu asamu tawul karami mai kyau asa cikin ruwa mai tsafta a dinga goge min jikina nan da wasu yan mintuna daga kafa har zuwa goshina
Na zaci tare da yaynmu zasu fita sai naga yaynmu ya zauna Babana da Anty Maijidda suka fita Anty tace bara na dauko tawul da ruwa a zatona anty ce zatayi min gugar jikin sai naga yaynmu ya amsa ita kuma ta fita har da kulle kofa..
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
yaynmu ya iso gabana ya tsuhunna sanye yake da rigar boyel fara tas kamshin turare sai tashi yake a jikinsa ya cire farar hular shi ya ajiye sannan yasa hannuwanshi ya jawoni yaja zif din rigata kasa gabana sai faduwa yake tsoro da mamaki suka cikani a raina nace yaya zasu ce yayanmu ne zai min wannan aiki to ko dakinmu daya ai bai dace ba inaji ina gani ya cire min riga da breziya ta daga ni sai zani iya cibiya sannan yajuyo dani naso in sa hannu in kare kirjina amma kasancewar jikina babu kwari sai na kasa dan haka sai na runtse idona ina jiran naji ruwan a jkina sai naji shiru a hankali na bude idona yaynmu na gani a gurin da yake idonshi kyam a kan Kirjina da sauri nasa hannu na rufe ya dauko tawul din ya soma goge saman cikina zuwa kirjina sannan fuskata duk da yayi kokarin kamewa dan kada na gane na fuskanci ya dimauta da ganin halittar kirjina haka yafi goge min gurin can aka kwankwasa kofa ya yi sauri ya samin riga sannan yace a shigo, likita ya shigo da magunguna yace a bani

abinci naci sai nasha ynxu,bayan tafiyar likitan ne yayi ma Anty Maijidda waya a kawo min ruwan Tea, su da yawa suka shigo Anty Maijidda da Anty Yagana,Mami Amira harda tsohuwa kakata sun min sannu sannan suka fita,a raina nace a rasa mai bani tea dinma sai yaynmu kadan na sha nace ya isheni ya harare ni karbi da sauri na karba na kafa kai na shanye yace ko kefa,kafin ya rufe baki sai amai na wanke mishi jiki tas da amai yana rike dani sai da na gama sannan tsoro ya kamani na tuna Mami ta taba bani Ibr wai wata rana Bilkisu bata da Ify tayi amai a dakin Haj Yaya ya shigo ya taka sai da ya mareta duk da bata da Ify wai ya zatayi amai a daki da sauri na dube shi cikin tsoro nace yi hakuri dan Allah......shiiii ya katseni sannan ya dubeni yace kin gama na daga kai yace Anty Maijidda ta shigo tana ganina tace ya kika ma yayanku amai kin bata mashi jiki Iman yace ba komai ta kuskure bakinta ta sha maganin yanxu zanje gida na dawo anjima, bayan na sha maganin na kwanta kawai sai barci, bani na farka ba sai magriba Anty Yagana suka sani nayi wanka sannan naji suna cewa tun da jikin da sauki a kaita tayi sallama da mamanta,na dubi Anty nace dan Allah Anty Maijidda bani da Ify kar ku kaini wani gurin suka ce naje naji sauki a dakina ina kuka ina komi suka kaini gurin mamana tayi min nasiha mai ratsa jiki sannan ta kara da cewa tsafta da girki suma manyan makamaine na kara karfin zaman aure dana haka ki kula,yan uwan mama da suka zo da yan uwan Maska,dangin Alhj suma sunyi min tasu nasihar amma har ynxu banji wanda yace min ga mijin ba gurin Alhj aka kaini shima yayi min nasiha sosai har ya kara da cewa duk wanda kika gani a matsayin mijinki to kiyi mishi biyayya haka Allah ya tsara ni dai sai kuka nakeyi,mun taso tsakar gida,gidan cike yake da mutane yawanci dangin mama ne da kawayenta daga nan sai gidan kawu malam shima yayi min nasiha sosai kuma yace min na rike mijina haka Allah ya hukunta,Bamu shiga cikin gidan ba da yake su Baba suna can gidan mamana gidan babana muka koma a gurguje kafin motar daukar amarya tazo suka kuma min wani gyaran na dubi Amira da Mami nace ina wayata suka ce tana gurin Saudat suka kirata ta kawo min na kunna ta ina budeta text ne ya fara shigowa na bude shi naga ansa

"dama nace miki i am always lucky gashi kuma.. kaina ya daure nace me kenan sai naja tsaki na soma del din text dinshi nace koma wanene ya karata can har yana cewa baga shi nan ba yana nufin shi aka aura min?me karya ina ma su Baba suka wani sanshi,su Mami suka ce ke da wa kike wannan fadan?na dan kishingida nace um Amira tace kinsan mijinki kuwa?da sauri na tashi zaune nace wanene Mami tace itama fa bata sani ba Amiran,nace um ni ko wanene ma na hakura zan zauna dashi tun da rufa mini asiri ma yayi bayan an kini kuma shima wanda ya kini din dama bashi zuciyata take so ba na rasa wanda nake son ma na hakura bare Adams? sai naga Amira da Mami sunyi dariya nace in ma kun sanshi baku son ku gaya min ai zan ganshi ne,suka ce har ma ku zauna har abada,muna cikin haka Anty Maijidda ta shigo tace Babana yana san ganina ina zaune gabanshi yana mini nasiha gami da nuna min nayi biyayya nayi koyi da hali irin na uwata sannan yace yaji dadin mijin da Alhj ya zaba min domin shi kansa lokacin da ya ganshi ya so ace ya kasance mijina,na soma kuka yace na daina kuka duk abinda nake bukata kar na zama mai rokon mijina na mishi waya zai bani kamar na tambayeshi wanene mijin sai naji kunya nayi shiru,mamakin da naji shine ganin abokan yaynmu sune dai suka zo daukar Amarya,a motar Isma'il aka daukeni a raina nace to ni Iman me ya kawo yaynmu kai amarya kuma?to ko dai Adams din ne tsokanata sukeyi?wa zan samu ya amsa min wadannan tambayoyi?ina cikin tunani har muka iso gidan,Anty Yagana ke rike dani fuskata rufe har cikin gidan ta umarceni dana shiga da kafar dama gami da yin Bissimila nayi yanda tace tafi tafi har dakina inda ta zaunar dani akan gado nan da nan mutane suka cika gidan yan ganin daki nan na bude idona tsayawa fadar kayan da aka zuba min a dakin ai kauyanci ne komai na dakin green ne bedroom din kenan falon dai ban fita ba hatta setin gadon dasu madubin duka green ne,ban taba ganin setin irin setin nan ba haka kowa yake cewa Mama,Mami ta shigo ta dubeni kai Iman kin more kaya kinga falonki da bayinki kuwa?Amira tace ai kallo yana kicin nace uhm! ina bayin suka nuna min gashi nan ashe ma a cikin bedroom din yake haka dai mutane sukayi ta zuwa suna leka bayi da sauran wurare har

suka soma tfy
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Ya rage sauran kawayena,Nasir ma yayiwa Mami waya wai ta fito su tafi ta dubeni matar yaya sai kinji ni a waya da sauri nace wanne yayan?ta fita tana dariya Amira ma ta fita tana dariya, tace to Iman sai ki ganni dan wannan mijin naki baya wasa da mutane bare muce zasu shigo da aboka ango na riketa nace sai ta gaya min ko wanene tace bansanshi ba na dai ganshi dazu ne naga kamar ba shi da fara'a,ta kwace nace dan Allah Amira kada ki tafi ko saurarona batayi ba sai da ta kai kofar fita daga bedroom din sannan tace Anty Yagana tace in ce maki sun wuce sai sunzo kawo maki akwatuna amma akwai kaya cikin wardrp nace shine suma suka gudu harda Saudatu,Amira tace eh na taso nace bari na rakaki da gudu ta fita kamar dama ta san riketa na so nayi tace sai wata rana har falina na fita tausayin kaina ya kamani nan tsakiyar falon na tsaya ina duban dukiyar da iyayena suka narkar cikin katon falon komai na ciki tunda ga Carpet har zuwa Kujera Labule marun ne,wata yar kofa na gani koda na bude ashe kicin ne ya tsaru kayan aiki masu amfani da lantarki gasu nan,na dawo na daga labulen window na leka sai naga wani katon falone na alfarma falon da kamar naso na sanshi a hankali na bude kofar dakin na leko gabana yayi wani mugun faduwa ganin gidan yaynmu tabbas gidan yaynmu ne kenan shi na aura wata zuciyar tace min ko Kabir ne,shine zamu zauna anan kafin ya gama gida?na koma bedroom kaina daure na leka Toilet din da naji ana ta kwarzanta koda na ganshi sai da nace Allah yasa ka ma iyayena da albarka na shiga nayi alwala nazo nayi shafai da wuturi da yake nayi isha a gida na idar na bude wardrof na ga kaya kala kala kusan cike na dauko rigar barcina mai hawa biyu nasa na kama gashina na tufke sai a lokacin na kula da wani show glass cike da kayan kwalba a cikin kwalban akwai turarukan wuta masu kamshi,na hau gado na kwanta zuciyata cike da tsoro da tunanin

wa na aura ga tsoro ni kadai ce dan da na saba ni dasu Jamila muke kwana nace gobe zanyi wa su Jamila waya su dawo nan,can barci ya soma daukana naji motsin kofa da sauri na juya don ganin mai shigowa .Yaynmu na gani tsaye cikin kayan barci riga da dogon wando kyanshi da annuri yana tashi a tare dashi ya taho a hankali har kusa da gadon nima na tashi zaune fuskarshi babu yabo ba fallasa yace ya jikin?a hankali yake magana,da sauki na fada ina dubansa farin ciki da dadi suja cikani sai dai na kanne,yace ina yake maki ciwo ynxu?nace babu yace shi kenan sai da safe nace Allah ya kaimu ya juya na bishi da kallo yana fita na fda kan gadon don murna da farin ciki sai na nemi ciwon ma na rasa kai a karshema durowa nayi na shiga bayi alwala nayo nazo nayi ta nafilfili ina ma Allah godiya daya sa iyayena suka zaba min abin sona,shiko daya koma dakinshi sai da ya gama komai na al'adar rayuwarshi sannan ya dauki waya ya kira layin Mimi ta dan jima tana ringin sannan ta dauka,lafiya?abinda ta soma tambaya kenan,ya baki kawo min lipton ba ne? tace Amarya ba sai ta kawo maka ba ta kashe wayar ya jima yana duban wayar shi mimi zata kashe ma waya?lallai ma, da kanshi ya shiga kicin din ya dafa ya fito bayan ya gama ya kwanta ya jawo filo ya rungume tsam a kirjinshi idanuwanshi a lumshe ido surar Iman kawai yake gani,gsky ya girgiza da ganin halittar kirjinta bai taba tunanin haka take ba wato shi wannan abu baiwa ce daga Allah ba shekaru ne ba domin ko yanzu tafiMimi kira duk da dai kirjin kawai ya gani ranar yayi baccin da ya jima baiyi ba tunda ya samu yarinyar daya jima yana so gashi tana da abin da yafi so a gurin ya mace duk biyun wato kasa da sama sai dai inda zai samu matsala yaya zai yi ya tinkareta da wani batu na bukata?a ganin shi sai girmanshi ya zube a idonta da wannan tunani yayi barci.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-
Novels-389304544597988/?
_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Da safe nayi wanka na gyara gado na share na goge inda yayi datti sannan na jona naurar saka turaren wuta

na zuba nan da nan dakin ya gauraye da kamshi kwalliya na sha cikin atamfa yar Ghana dinkin riga da siket rigar fitet Breazier style gashi na na daure shi da ribon sannan na daura dankwali turare na fesa na koma falona na shiga kokarin hada TV,ban ji karar bude kofa ba sai dai naji sallama gabana ya fadi na juyo yana tsaye da Jeans baki da shirt,yayi kyau sosai na zauna kan kafet na ce ina kwana?ya amsa Ify ya jiki?nace naji sauki ya juyo tare da fadin zo nabi bayanshi har falo ya zauna kan kujera sannan yace shiga dakin Mimi ki gaisheta sannan kice tazo ina kiranta cikin tsoro na shiga tana kwance a kan doguwar kujera cikin ta ya tsufa girman falonta kamar nawa nace Anty Mimi ina kwana da sauri ta tashi ke!! Ta daka min tsawa ni ba antyn ki bace batun kwana kuma banganshi ba cikin tsoro na ja baya nace yaynmu yace kizo ban jira amsa ba nayi waje da gudu ya dubeni menene?nace am....ba komai yace to zauna nan ya nuna min kujerar da take kalonshi kusan minti goma sannan ta fito kusa da shi ta zauna tana wani cin magani yace kinsan tun dazu nace ki zo shine kika ki zuwa ko?ta kauda kai taki magana yace to dama nayi kiranki ne dan na gabatar miki da Amina wato Iman a matsayin yar uwa.....ta katse shi ni ba yaruwata bace ya ce to ya isa haka ni matata ce kamar yanda kike matata tace to kace dama can kana sonta munafunci ne kawai.....ya mike yanda uwata tace in aureki haka na aureki ke ma zabin mahaifiyata ce kin gane?wannan kuma ya nuna ni zabin mahaifina ce dan haka ba zabina a cikinku sai ku kula na san gaba kila na samo zabina. kuma kina cin albarkacin cikinki ne,ya fita gsky naji haushin abinda yayanmu yace ko da yake Anty Mimi ta fini jin haushin tunda ya ba da ita gabana.

Da rana bala dryva ya kawo mana abinci inji Mama,yaynmu ya dawo lokacin ina kwance a kan kujera a falona na sake wanka na sanya material baki me zanen fararen fulawoyi ya zauna kan kujera na tashi zaune sannan nace sannu da zuwa yace yauwa na mike na shiga kicin na zubo mishi kayan ciki salat ma kadan na zuba mashi na hado da coke da ruwan cway na ajiye a gabansa nace mama ce ta aiko yace to kin ba mimi ne?nace a'a yace bari na kai mata wannan mamaki ya kamani a raina nace ita ba tayi ta bani ba

sai ni na ce da saura bari na kai mata yace kawo dai na kai mata nace to na shiga na dauko na kawo mishi ya fita jim kadan ya dawo ina zaune shima ya zauna yana cin abinci yace kunna min TV nan na dubeshi nace ai ba'a hada area din ba sai dai kaset zan saka maka yace barshi sai da ya gama na kwashe kayan ya dan kishingida yace Iman kina jina?nace eh yace kar ki yarda na samu Ibr kin ma Mimi rashin kunya sannan ki dinga yin abinci kullum kina bata saboda kinga tana da ciki sannan zansa Mama ta samo miki mai tayaki aiki kin gane ko?nace eh bama sai ka nemo mai aiki ba ni zanyi,yace shi kenan yanzu Babanki ya cika mana Store da kayan abinci gami da kayan cefane sai ki duba babban kicin duk abinda babu sai ki rubuta Kabir zai kawo nace to ya mike ya fita na bishi da kallo a raina nace dama nasan mai aiki zan zama a gidan nan.
Yayanmu zaune a gaban Haj Yaya san da yazo ya sameta tana ta sunturi a daki abin duniya ya taru ya mata yawa, in da ta san danta zai auri matsiyaciyar yarinyar nan da bata kashe kudinta a banza ba gashi kuma abinda ya faru tana kishi da uwarta sannan yarta ta aure ma ta danta kuma wanda ta fi so; bazata yiwu ba ta ta tada masifa Alhj yace zai saketa in har ta sa dan nata ya saki Iman,ita kam ba zata iya hada zuriya da Habiba, ta dube shi wacce shawara ka yanke a kan yarinyar nan?gabanshi ya fadi yace to Haj ni ya zanyi haka Allah ya kaddara.....ta dubeshi haka ka ce?yace to ya zanyi ne Haj kina jin fa abinda Alhj yace ki kwantar da hankalinki bana son ace ta kaina kun rabu tace to naji amma sai ka min alkawari ba zaka kula yarinyar nan ba dan gsky ba zan so hada zuri'a da Habiba ba,yayi shiru na dan lokaci can yace to Haj shikenan? tace in har ka min haka shi kenan kar ka yarda ka saurareta dama kayi ta mata wulakanci in sun gaji suje su dakkota yace to duk zanyi tace to yawwa Allah yayi maka albarka,ya fito yana nazarin yanda zaiyi.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Shida daidai na yamma na gama dafa abinci gidan sai kamshi yake na zuba ma Baba mai gadi da direba na fita na mika musu,ina fitowa wanka akayi kiran sallah sai dana yi isha'i sannan nayi kwalliya, paper less nasa yellow nayi kyau sosai na fito yana zaune a falona nace sannu da zuwa yace yauwa kin kaima Mimi abincinta ne?a'a ban kai mataba na dauka sai ka shigo amma bari na kai mata yace kawo nan in bana nan kika gama ki kai mata nace to na kawo mishi ya dibar mata komai ya fita,nace kai auran mijin wata ko matsala, ya dawo zo muci ai naci yace shi kenan daya gama ya fita sai misalin tara ya min waya na dauka yace na dafa mishi lipton zai zo ya dauka na dafa mishi mai kayan kamshi da tafarnuwa kadan a falo na ajiye mishi na shige dakina na kwanta.
Haka naci gaba da zama tamkar yar aiki kullum da safe inyi gyaran dakina da falona in gyara babban falo na hada Break fast na gyara kicin ban dai taba gyara mishi daki ba ban ma taba sanin yanda dakin yake ba,inyi abinci da safe da rana da yamma wataran ma har Anty mimi tace bashi take so ba yaynmu yace in sake mata wanda takeso, duk aikin da nakeyi bai taba damuna ba tunda na riga na saba saidai bai kai wannan ba kuma nasan lada nake samu batun kulani da yaynmu baiyi ba ko a jikina tunda dama ni tsoro nakeji.Ina da kwana shida su Anty Yagana suka zo suka kawo min akwatuna har na gurin Adams, yaynmu dai bai min akwati ba sadakima babana ne ya bada.
shina na ashirin da hudu Anty Mimi ta tashi da nakuda cikin dare misalin karfe biyu Yayanmu ya kwankwasa min kofa na bude cikin tsoro yace nazo muje Asibiti Mimi batada Ify da sauri muka tafi ya uzzura min da na fito mu tafi gyale kawai na rufa a kan kayan barcina riga da wando shi ya kaita cikin motar sannan na shiga na riketa sai fizge fizge takeyi tana kuka takasako salati,muna isa aka shiga da ita dakin haihuwa,jim kadan suka ce ta kusa mu kawo kayan haihuwa inji likita, yaynmu ya koma gida ya dakko abubuwan da likitan yace mishi,sai shida na safe ta haihu,san da suka zo mana albishir yaynmu yana masallaci sai ni suka ce min an samu namiji murna na dinga yi na kosa yaynmu ya dawo sai da ya dawo sun zanta da likitan na tare shi da murnata nace yaynmu Anty ta haifi Baby

boy da murmushi yace alhmdll ina take?nace tana ciki ina kallon likitan ni ya kura ma ido nurse suka fito da yaron ni na soma daukanshi kyakkyawa yana kama da yaynmu sai dai farin mamanshi ya dauko,yaynmu ya daukeshi yana mishi addu'a likitan ya matso yana taya yaynmu murna ya dubeni kema sai ki kokari kiyi aure ko kin samu naki babyn,duk da murnar da yaynmu yake sai daya gimtse fuska gami da cewa naje na zauna na koma kan benci na zauna can aka fito da Anty Mimi zuwa dakin hutu,can ya dawo ya sameni zaune fuskarsa a daure yace min na tashi ya kaini gida yaje yayi waya su Haj zasu zo, dama dan bai zo da wayoyinshi bane muna mota yace shi ne na fito da kayan barci dan wulakanci ba ko hijabi naxo ina ta dariya a gaban doc,nayi shiru to me zance?shine fa ya uzzura min na fito na fito don tsoron masifarshi ne ko zani ban tsaya rubawa ba yace ina miki magana kinyi min shiru ko?na rasa me zance masa sai nace to kayi hakuri.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Tunda aka yi haihuwar nan ban zauna ba dama ranar aka sallame su kullum gidan cike yake da yan zuwa barka girki nayi masu sau uku sau hudu, ga habaicin su Anty Mariya da sauran kawayen mai jego gyaran gida har dakin mai jego sani sukeyi ina jin tsoron su ba zan ce bazanyi ba, ana sauran kwana biu suna ranar na sha wuya bugun fulawa suka jingine na cincin da doughnut kuma yan uwanta ba su sa hannu ba daga ni sai Mami sai ko matar Isma'il abokin yaynmu sune suka tayani,ga aikin gida da kyar nayi sallar isha'i na shiga bayi na gasa jikina na fito na kwanta na manta ban daf mishi lipton din nashi ba barci mai nauyi ya daukeni cikin barci naji ana tashina ni uwar yan tsoro na tashi zanyi ihu ya toshe min baki da tafin hannunahi yace ke sarkin tsoro ni ne ganin yaynmu nayi ajiyar zuciya yace ina lipton dina?gabana ya fadi nace na manta ne yace to na tuna maki ya juya yayi waje haka na tashi na dafa mishi jikina na ciwo. washegari ya dawo da

yamma ina falo ina gyarawa ya shiga dakin maijego ya shiga suna bedroom suna ta tsuga Ibr tana basu Ibr yaynmu baya kula ni tun da nazo gidan bai taba kwana akina ba sai dai aiki kamar jaka ai bari a gama suna har kashin baby ita zata wanke, shi yana falo yana jinsu ga Anty Hadiza tana sallah a falon ba dama ta yanke tace su daina, tana tayi kawaye da Anty Mariya suna zugata, can yayi sallama ya shiga sai suka yi shiru suka daina maganar yaba ta kayan dake hannunshi ya juya dama kayan fitar suna ne yayi mana kala shida shida yayi mana, dakina ya wuce na aje tsintsiyar na shiga kicin dina na kawo mishi abinci gami da mishi sannu da zuwa na koma ga aikina na barshi nan yana cin abinci yana kallon TV.
Ranar suna ko tun asuba na tashi na shiga kicin,dama yaynmu yace zaizo da abokanshi da safe suyi walima anan kafin mutane su soma taruwa dama nayi redin sinasir da mai na sai farar shinkafa da miyar anta sannan na dafa masu ruwan lipton mai kayan kamshi cikin katon fulas nasa ,farfesun kan sa sai peape mit na naman rago, bakwai da rabi na gama aikina, da yake a babban kicin nayi aikin.Nasuna kuwa ta ba kawayenta ne suyo daga can suzo dashi,ina shafe shafe bayan na fito daga wanka yaynmu yayo mani waya wai gasu nan zuwa,shadda galila yar gaske cikin kayan Adams take ta sha aiki kalar pink ni kaina na san na hadu, na zuba gwala gwalai na wuya da hannu har da kafa na baza turare sai kamshi nake zan fito yaynmu ya shigo sai mukayi karo dif yayi yana dubana shima yayi kyau cikin lallausan blue din yadin shi cikin murya kasa kasa idonshi a kaina yace kin gama?girata na daga alamar eh yace to sai ki kawo mana ya juya,darduma katuwa na fito da ita na nufi gurinsu,suna da yawa cikin ladabi na gaishe su sannan nace bari na sa maku wannan a kasa zaifi ko?na fada ina duban yaynmu fuskarshi ba a sake ba yace to bayan na shiga gidane na koma kicin ina fito da kayan abinci sai da na gama fito da kulolin sannan na kawo plate plate da cokula da kuma kofuna na kawo drinks da sugar da madara ko mai dai dai na shan tea
kusa da yayanmu na tsuguna dan na sanshi yafi son komai a mishi na zuba mishi tea sannan na sa mishi sinasir da miya na dau karamin plate na sa mishi

farfesu na tura gabanshi,Isma'il yace duk kai kadai? Nasir yace ka san yan kwallo da mugun ci shi dai baiyi magana ba na jawo wani plate din yayi min wani kallo kasa kasa sannan yace a hankali bar nan,na tashi zan wuce Nasir yace au mu da kanmu zamusa?Maska mufa baki ne?yaynmu ya dauki kofin tea ya soma sha yana fadin to kar ku zuba da kanku tun da cikin wani zaku zuba ya dubeni da sauri na wuce,Ismail yace Maska kana takurawa yarinyar nan dubanta kawai kayi amma da sauri ta bar gurin yace to ni bani son raini kuma ka sani Nasir yace ta raini ai ta kare tunda yanzu taga girman naka ko yaya yake Maska yace ba tonan asiri ba ni bata ga kalar girmana ba suka sadariya Bello yace kayi kokari kana da mace kamar wannan ai sai godiya haka suka yi ta hira.
Gidan dankam da mutane muna falo ni da Mami tace kai Iman kinyi kyau sosai wannan dinkin ya amshe ki nace me? tayi dariya sannan tace shi kenan tunda baki gane ba nifa ba abin da nake a gidan nan sai aiki kumani bai dameni ba, Mami ta gyara zama ta ce kina nufin kallonki yaynmu ke yi? nace kallon ma ban isa ba Mami tace lalai ynxu ke kin sa mishi ido?nace cab ji Mami da wata magana ni ban ma san dadin abin ba bare nace zan kai kaina ai ko na san komai ba zan mishi ba ina mace Mami ta tashi ta jawo jakata ta ciro wata yar kwalba ga wannan ki biya dubu uku,na menene?tace ke ce zaki bani Ibr kinga amfanin sa sai zaki kwanta sannan ki shafa kadan dan dis zaki sa a tafin hannunki ki shafa yana da tsananin kamshi?nace yayi dubu uku Mami tace aikin shi yafi dubu goma zaki fahimata in dai yaynmu ya shaki kamshin,na ce ai ba tare muke kwana ba tace ke dai kamar ba mace ba ke ba zaki yi sanadin da zaki gifta ta gabanshi ba?nace to ai bani da kudi Mami tace sai fa kin sai wannan turaren yar arab take kawo mana har ma da wasu sai kin shigo gari zan hadaki da ita nima fati matar Ismail ce ta hadamu na amshi wata kwalbar idan tazo gobe ta tashi tace bari na gaida Bilkisu tana fita na shiga daki wato bedroom na jawo durowa nasa kwalbar a ciki sannan na shiga toilet alwala nayi nayi azahar sannan na cire kayan da ya mana na daura zani ina warware riga ya shigo a kan kirjina ya saukar da idonshi nayi sauri na sa rigar

In kin gama ki samin ruwa a toilet dinki mutane sunyi yawa a hanyar dakina ya koma falona ni kuma na hada mishi ruwan wanka ya shiga toilet ni kuma na koma falo yana daga ciki ya kirani Iman nace na'am nazo yana duban mirror yace kije dakina ki dakko min kaya nace wasu kala?ya dubeni ke baki san dukkan kayana kalar da nake so nake saya ba?dan haka kowanne ki kawo min,ina murda kofar ta bude yaune karo na na farko da na shiga dakin nan na tsaya kallon dakin tunda ga kan kafet labulayen milk ne katuwar katifa ce irin wadda ba a sata a gado din nan zanin gadon shi ma milk ne dakin ba wani tarkace amma ya tsaru gurin kayan nashi na nufa bayan na ciro mishi marun sai hula da takalmi ina fitowa su Anty Mimi suna hoto a nan babban falo cikin tsoro da mamki take kallona na shige abina ya ce to ina singlet da gajeren wando?na koma na dauko masa falo na koma ya shirya yana fitowa a raina nace munyi anko,ya dubeni zanfita nace bazaka ci komai bane,no am ok nace a dawo lfy ya fita,naji dadin yanda yaynmu yayi ya nuna wa yan sunan ina da daidai nawa matsayin haka suna ya tashi yaro yaci sunan kakanshi,Baban Anty Mimi wato zaidu sai suna kiranshi daddy,a daren na kudiri aniyar amfani da turaren nan na nufi baya bandaki bayan na gama komai nayi wanka kalolin turaruka na shafa ga wani turare da anty yagana ta bani wai tsugunna duk sati ban taba amfani dashi ba sai yau,na dakko na gurin mami ina budewa bisa ga tsautsayi sai kwalbar ta subuce a jikina kusan rabi ya zube na rufe sauran ina ta tsaki nace dana san zubewa zaiyi da ban saye shi ba rigar baccin dana sa doguwa ce mai gidan breziya tana da santsi sannan bin jiki takeyi ban saka komai ba sai pant dan haka turaren sai ya manne min a jiki,waya yaynmu yayi min wai na kai mashi lipton dinshi dakinshi, gabana ya fadi sai na sa hijabin sallata na nufi dakin fitilar da ta haske dakin blue ce kuma mai duhu sannan ta kawo ta dauke haka takeyi, yana zaune kan sallaya ya shafa addua sannan ajiye kizo kiyi alwala nace ina da alwala yanzu nayi shafai da wuturi,raka'a biyu mukayi bayan gama adduoi ne yayi min tambayoyi game da ibada na amsa sannan yace na jira shi yana zuwa ina nan zaune ya fita jim kadan ya dawo ya dubeni cire hijabin kizo ki zuba min a kofi ,fuskarshi a daure yake magana dan

haka tukunna ina zuwa ta fita sai dakinta,layin yaynmu ta kira tana tambayarsa abinda yake faruwa yace mata ba komi dama yana sonyi sallama dani ne kuma na kulke kofa naki na bude,mama tace yayi tfyrshi yace ba dama na tafi ba tare da nayi mata sallama ba,mama ta samuAllhj ku saukeni gidan Iman din dan nayi waya da yaynsu ynxu bansan me ake ciki ba.sai naji waya tana ringin na tashi na dauka sunan mamana na gani na dauka nace mama,tace bude min kofa,Jikina ya soma rawa gabana na gaduwa nace to ina bude kofa mama ta shigk yaynmu ya biyo bayanta kafin nayi magana sai jin saukar mari nayi gau!mama ta sakar min gami da fadin ashe baki da mutunci?kin kama kofa kin rufe ashe kece ma mijin?haka na koya miki?ko haka kika ga inayi?ni kam sai kuka nakeyi ta kuma tasowa tana kokarin cire wayar cd na ruga bayan yaynmu ina cewa mama kiyi hakuri ba zan sake ba na daina yaynmu yace Maman Sagir kiyi hakuri bafa wani abu tayi min ba kar ki doke ta kiyi hakuri mama tace ai sai naga ta baka hakuri da sauri nace yaynmu kayi hakuri ba zan kuma ba yace na hakura dama ba wani laifin kirki bane,mama tayi waje ta tafi na fada kan kujera ina kuka,yaynmu yazo ya rungumeni ta baya yana ce min kinga kinsa mmn Sagir ta bugar mani ke ko?cikin kuka nace ba kai bane ka kirata ba ni abinda kayi min ban fada ba sai kai ne kaje ka fada mata yace no ban fada mata ba ban san yanda akayi tajiba,naci gaba da kukana, wayar shi ta soma ringin ya dan sakeni ya ciro wayar a aljihun jeans din shi ina jin shi yace mimi menene?ina zuwa mana haushi ya kamani na mike na nufi bedroom kan gado na fada ina kuka ya shigo ya jawoni jikinshi yana fadin na gaji da fushin da kike yi dani ki fada min wai me kike so nayi miki?ko meye fada min zan yi maki indai zaki huce, yana magana hannunshi rike da fuskata yana kallona ido cikin ido yace gaya min ko in ciro kaina in baki?hawaye suka zubo daga idona yace bana son ganin hawayenki fa ya dkra harshensa a kan lebena yana zagayawa dasu a hankali ya isa har bakina gsky yayi missn dina a lot nan da nan ya rude cikin kankanin lokaci ya rabani da kayana ya shiga sarrafa albarkatun kirjina sai da na ga ya gama fita hayyacinsa sannan na janye jikina na koma gefe na kudundune guri daya a wahalce yace menene kuma?na soma kuka yace

oh my God kar ki min wannan horon pls cikin kuka na ce baka ce in jika abina insha ba,sorry da wasa nake maki,ya iso gurin ya jawoni zo in sha miki ai ke na san ba zaki iya sha ba,ni zan sha miki ko?haka yayi ta ribatata gami da lallashina kauna da soyayyar shi din nan mai tsada ya nuna min na sha wahala a ranar a hannunshi tun ina yin kawaici sai nima ban san sanda na ba da kai ba
Yaynmu kenan zuma neshu,ga zaki ga harbi,bayan lafawar komai sai ya kwantar dani saman cikinshi yana cewa Iman kin yarda in tafi ko a'a?in kince kar na tafi na zauna fuskata a tamke nace ni zan hanaka tfy?to mu tafi duka,ni ba inda zani yace fada min me kike so? nace ni makaranta nake son shiga yayi shiru na wani lokaci sannan ya kara rungumeni tsam har ina murna na sha zai ce ya amince amma sai naji yace Iman ki cire maganar krt nan na gaya miki kin bar daman ki tun baya dan haka ynxu ki daina wannan batun,cikin muryar tausaya nace dan baka sona ko?haka Aunty Mimi da yake kana sonta ai ka barta tayi a cikin turawa ma yace kin ga ita tana cikin karatunta na aureta bayanda za'ayi na hana ta kema da kinbi shawarata a wancan lokacin da kinzo kina krt haka nan zan daure na barki ki karasa amma ynxu u a too late sai dai kiyi hakuri in da wani abin da kike so sai ki gaya min ko menene ynxu zan maki shi sannan ki daina cewa bana sonki a ganina kauyanci ne in tsaya ina fada maki irin son da nake maki jikina da idanuna in kin duba sun isa ke abinda ma kike min in wata ce da sai ta gane kuskurenta ynxu tashi ki shirya zaki bimu ne?nace ni fa ba zanje ba haka yayi ta lallashina sai da ya ga na dan sauka sannan ya nufi dakinshi dan yin wanka,Aunty Mimi dake zaune a falo tana ganinshi sai ta mike tana fadin Honey wannan wane irin wulakancine, daga ka shiga sallama har nayi wanka na shirya baka fito ba da ace ni kake jira da ynxu ka hau fada da yake....ya katseta ynxu sai ki jirani nayi wanka ya wuce ta bishi,wanka? wanka fa kace?tana tsaye dakin ya fito ta dube shi tabbas wanka yayi ta ce lallai dan jaraba da masifa an shiryama sai da aka tsaya fitina,ya dubeta ke dawa kike?tace wanda ya tsargu yace to inma dani kike ai ba zina nayi ba,tace aikin banza in kuna son ku burge sai ka tasa ta a gaba ku tafi tare yace ai dan tace ba zata

bane,fushi da takaici ya kamata ta dube shi tace to nima na fasa zuwan sai ka tafi da ita yaja tsaki yace to ai ni da zuwanki da rashinshi duk daya ne dan banbancin kadan ne kina can ma ba abincin kikeyi ba komai ni nake ma kaina kwanciya kawai ke hadamu an ce miki ke kadai nake aure?haka suka ci gaba da hayaniya ni ban sani ba ina daki na fito wanka na gama saka kayana kenansai gashi, bai min magana ba kai tsaye ya wuce gurin ajiye kayana ya shiga fito dasu kusan kala biyar ya jawo jakar tfy ya zuba takalma uku sai kayan shafe shafe na kan madubi na ya diba ya zuba fuskarsa a murtuke tsoro ya kamani na sha zai maidani gida ne ya sakeni,ya dubeni tashi mu tafi cikin tsoro na ce ina?tsawa ya daka min tashi mana jikina na bari na dauki hijabina na bishi ya kashe kayan wuta na fito yaja kofa muka fita muka hau motarsa yaja sai da mukayi nisa sannan ya dauki wayar shi ya kira yaya Kabir ya tambayeahi yana ina ne?yace yana gida yace mu hadu airport ka karbi mot,Kabir yace ynxu ma haj tace in zo in kaita gidanku naga Mimi tazo wai ka bugeta yace shareta Kabir Haj kuma kace mata na wuce,ina ji ban tanka ba abinka da aikin kudi nan da nan akayi mana komai na tfy har kabir ma yazo suka ta kai kawo har komai ya kammala sai gani tsuru a jirgi, tfy ta tafo sai gani a England, tun da muka sauka motar club din su ta zo daukar mu,ashe gidane na gani na fada,bayan na tashi daga barcin gajiyar hanya nayi wanka yaynmu baya nan na sa riga da siket na less,ya shigo da ledoji,kin tashi big girl nace ni ce big gal? tsokanata kawai kakeyi,yace ai kin ma fi big gal zoki ci abinci nasan yunwa kike ji ko ,muna ciye ciyenmu yana tsokanata da yan wasanni,rayuwarmu abin sha'awa, tun safe nake tashi lokacin yanagurin motsa jiki,inshiga kicin in hada mana break inyi wanka,kwalliya sosai nakeyi cikin kananan kaya in same shi daidai san da yake motsa jiki karfe takwas,ina shiga zai ce big gal kinyi kyau,in gabatar mashi da abin ciye ciye,Lipton yake fara sha sannan yaci sauran kayan ciye ciyen, sai yayi dam sannan in hada mishi ruwan wanka,da ya fito sai na dauko masa jeans da sauran kayan da yake amfani dasu,in ya gama shiri sai yace nayi kyau big gal?sai nace kayi mana sai in raka shi bakin kofa.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu

nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Tunda nazo bai taba barina na fita waje ba haka baya bari nazo in wasu abokanshi sunzo sai na sa hijabina, in nace ya kaini yawo sai yace baya son mutane suna ganin mashini,shine yayi ma mama waya da baba yace musu mun wuce,kafin ya dawo da rana na gama abinci, haka in dare yayi bana wasa da cikinshi yaci muna hira tare da yan wasann,i in lokacin kwanciya yayi in sheka kwalliya tare da sa turaruka kala kala masu kamshi,bana sa komai a jikina in shige jikinshi mu kashe juna da sayayya. kafin sati nayi kyau, kullum da daddare in ya fita sai yazo min da kayan sawa kanana masu kyau takalma da kayan shafe shafe,ranar ina kwance ina kallo a falonmu sai naji ana kwankwasa kofa ina budewa sai naga Adams da shj da wata yarinya ta wuce sa'ata nace ku shigo ku zauna,suka zauna kan kujera sai da nayi hidima dasu sannan muka gaisa, na kula Adams baya son mu hada ido ko yana jin kunyata ne oho?nace Adams wannan ce madam din? yace eh itace sunanta Aisha, yau satin mu daya da zuwa,Maska yace min da ke yazo shine na kawo ta ku yi sabo ynxu zan barta anan saboda muna da wani zazzafan wasa karfe daya,nace to nagode,mun yini da Aisha har dare na fahimci tana da kirki ga saukin kai, tunda ta ga irin hidimar da nake shiryama Yayan mu sai tace tana son ta ma Adams girke girke amma bata iya ba ko zan yarda tana zuwa kullum ina koya mata nace babu matsala ta sanar da mijinta nima zan sanar da Yayan mu......
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Tawa Tasameni3-03
Posted by ANaM Dorayi on 09:47 AM, 09-Jan-16
Under: TAWA TASAMENI
__________NA HALIMA ABDULLAHI K/MASHI________
Mamidhaku da Aisha sosai cikin yan kwanaki, yau watan mu uku da zuwa kasar nan nayi kyau fata ta ta kara murjewa sai sheki da kyalli na keyi, komai na ya kara cika,na fito wanka na gama shafe shafena wani wando na sa iya gwiwa ya dameni,rigar bata kai cibi ba sannan wuyanta babbane dan duk albarkatun kirjina gasu nan a waje,ana gani irin kwalliyar da yaynmu ya fi so in yi mishi shi yasa baya shigowa da kowa sai ya shigo ya duba dan ya san ina mishi yanda yake son anina,ina kwance ina taunar cingam naji tsayuwar motar shi ta window na leka ya fito cikin blue din jc adidas da farin takalmi a kafarsa,ita ma motar kyakkyawa fara tas,samanta a budw daga nesa kamar ta wasan yara,ya sabo wata jaka adidas dince a bayansa, komai yaynmu yake yi ya amshe shi gashi mai kyau ina son guy din nan,tunanina ya katse sanda ya danna ,intercom na bude ya saki jakar yana kallona ni ko na juya na kuma juyawa a gabanshi nace nayi?ya rungume ni gami da fadin zaki kashe ni da salon gayun ki big gal,ina sonki nima na kankame shi nace nima ina sonka guy,muka nufi cikin gida,rayuwa kenan koda sunan wasa ban taba zaton yaynmu zai zama mjina ba. sai bayan babbar sallah muka soma shirin zuwa gida don bikin yaya Kabir Amira kam anyi nata, ban so bana nan ba sai dai alkawarin zanje yola gurinta
Mun fita dan yin tsaraba kudin da yaynmu ya zube min har tsoro ya bani, nayi kwalliya cikin suit riga da wando na sa karamin hijabi mai tsayawa iya wuya yayanmu yace kinyi kyau sai dai ba in sadaukar da jikinga ga wasu, canja, dole na sa siket da riga na jeans blue,yace saka abaya na saka yace kai itama tana nuna jiki sai dai muje na ringa kareki nace kai yaynmu ka cika kishi,yace na ji ba komai. Mun yi tsaraba sosai sannan mun zaga sai gurin sha biu muka dawo,a cikin jirgi ina lafe a jikin shi kamar mage yace saura yan mintuna mu sauka a kano nace to waye zai kaimu KD?yace akwai jirgi da zai je daidai sanda zamu sauka sai mu shiga,na ce amma gidan su mMama zamu ko?yace a'a gidanmu zamu nace kai yaynmu kai guy kaga nayi missin din

maMama,yace kada ki bata bakinki nace to ai da Aunty Mimi ne can kuke sauka sai ynxu na tuno da Aunty Mimi har gabana sai da ya fadi saboda tuno su da nayi,dana manta da yan matsaloli yace naji kinyi shiru ne ko da nike sauka a gidan dan saboda ke ne in ganki kawai amma ke sai ki boyewa ganina na dago ina dubanshi saboda ka ganni yace tabbas nace dama kana sona ne?yayi murmushi gami da kara rungume ni tsam! Kamar yanda kike sona muka yaudari zukatanmu ke ban san hujjar ki na kin gaya min ba amma ni hujjata na riga na cika baki gurin abokina bana son su min shakiyanci shi yasa naso kiyi karatun in kin girma sai in nuna ina sonki ,sai gashi kin nuna aure ki keso kika sa hankalina ya tashi(confession tym)karshe sanda na samu Ibr sa ranar ku da Adams naje Umara na roki ubangiji ya bani ke, ya amshi adduata cikin sauki ya bani ke lokacin da na soma yanke kauna da samunki,na kara shigewa jikin shi nace nima sonka nake guy tamkar raina yace kar ki rainani kar ki ga rashin girmana nace yaynmu ba raini tsakanin mu sai ma girmama da ka kara a idona.Muna ta hira har muka iso, muna mota nace yanxu yayanmu gidan ka zamu wuce?yace kina ganin zan yarda nayi missing dinki? jikina ba zai iya kwanciya ba in har bake.Muna isa gidanmu yaya Kabir yasa an gyara mana gidan tsaf, Aunty Mimi bata gidan nayi mamaki ban tambaya ba bayan munyi wanka mun ci abinci da mama ta aiko mana sannan muka fito sai gida.Munyi murna da ganin juna na shiga gurin Haj Yaya ta tamke fuskarta ko kallona batayi ba, na kari gaisuwata na tash,i da daddare muka koma gida.Haka akayi bikin yaya Kabir,mun hadu dasu Mami mun rungume juna,Mami tana da tsohon ciki ta ce kai Iman me yaynmu yake baki ne?kinyi kyau kin zama big gal ga wani class na musamman da kika kara nace Mami kinyi fa gsky Nasir yana kula mana dake,muka shiga dakinsu Jamil,a nan take bani Ibr rigimar yaynmu da Mimi, tayi mamakin da nace mata ban sani ba dan yaynmu bai gaya min ba,nace gsky naga bai taba kiranta a waya ba tun da muka je,Mami tace ki tashi tsaye ki dage da adduoi dan an ce suna nan suna shiga bokaye don su rabaku,wai kema da asiri aka aure ki wai duk abinda yayanmu ya ma Aunty Mimi ba yin kanshi bane asiri ne, nace su dai

sun kasa gane kaddara, Mami na san ina son yaynmu so daya tak amma ban taba tunanin zan aure shi ba dan na san cewa koda wasa niba ajin shi ba ce,to da da yake Allah ya kaddara da aure a tsakaninmu ana saura kwana uku biki Adams yace ya fasa Allah ya sani ban taba shan wani abu ko zuwa gurin wani dan yaynmu ya aure ni ba,Mami tace na sani kin san abinda mutane yakeyi,zai dauka haka kowa yake, tace saima kin ga Mimin duk ta rame, nace sun sa kansu a uku ni ban ma ganta ba,Mami tace tana nan ban ganta ba sai a gidan amaryanan muka hadu,gabana yayi mugun faduwa amma na dake tana ganina ta tafi,Dady ma gurin mamanta na hange shi.Zaune yaynmu yake a gaban Haj shi tana yi mashi fada akan abinda yayi wa Mimi ta kawo kara har da cewa yau din nan nake son kaje gidansu ka bata hakuri ta koma in ba haka ba zaka sha mamaki zaka ga yanda zanyi maka, ai ka bata min rai na karshe ka daketa sannan ka tafi abinka ba waya ba aike,yace yo ya take so ne haj? Ya Mimi take so dani ne? baki fa san abinda take min ba banda ke Haj da kike tsakaninmu da tuni ta koma gidansu ta koyo tarbiya in dai tana son zama dani,ya cigaba ke kanki ki dubi jikina wannan zuwan nafi kiba yarinyar nan da kika tsana tafi kula dani fiye da yanda ba kya zato gashi tana bin dokata tare da girmamani duk abin da nake so tana min fiye da yanda na bukata sannan.....ta daka mishi tsawa kai!.....ni dai na gaya maka in ta maka ina ruwana?ni dai nace kaje ka mai da Mimi yace ai bani nace ta tafi ba tace bana son wani kwane kwane, kaje ka maida ita yace shi kenan baru inje wanka,Bansan abinda ake ciki ba ina gida na gama gayuna yaynmu ya shigo nayi sauri na tashi na tare shi ina fadin yaynmu ina ka shiga ne?yace naje gida hadamin ruwan wanka nace ina zaka? Ba ka yi wanka dazu ba yace to ai ynxu tadi zanje na rungume shi nace gaya min gsky?ya sha mur ana wasa da maganar aurene?Na fada kan kujera nayi shiru ya zauna kusa dani tashi big gal kar tace ta fasa aure in shiga uku, nayi kicin a zatona da gaske ne nace cikin shagwaba ni ba zan hada ruwan wanka da za'aje tadi ba na turo baki gami da cewa to menene bana maka?gaya min na dinga yi maka kaji?na fada ina dubanshi sai ya fita yana fdin to ni bari naje na hada nayi ina nan zaune sai gashi cikin tattausan yadi milk

yayi kyau sosai na tashi da sauri na fisge key din motan na ruga uwar daki da gudu na wurgashi bayan gado ya biyo ni big gal ki bani key dina na shiga toilet na kulle na gaji da jira ya tafi.Ina girki duk raina a jagule na son ko wacce yarinya ce zata so yaynmu dan ba irin mazan da za'a kisu bane shi kam wancan lokacin yana gidan su Aunty Mimi, bayan ya faka da mota sai ya kira ta a waya sau uku tana tsinkewa sannan a na hudu ta dauka yace ke ana miki waya kin ki dauka kar ki raina min hankali fa,tace gidan bakonka ne da ba zaka shigo ba?ta kashe wayar yayi kamar ya juya sai kuma ya fasa dan ya tuno da Haj, yasa kai cikin gidan tana zaune a falo ddy yana barci a kan carpet,Haj Laure tana waya,ba wanda ya amsa mishi sallamar da yayi ya sami guri ya zauna,Mimi tski kallon inda yake a karshe ma sai ta tashi tayi ciki abinta ya dubi Haj Laure yace momy ina wuni? fuskarta a murtuke ta ce Ify lau ,yace momy nazo ne mu tafi gida da Mimi, tace eh da yake babyn wasan yara ce Mimin dole kace haka to ba zata koma ba sai naji dalilin duka da kana son ka tafi da gimbiyar taka ai ba sai ka daketa ba in kace ba zaka bita ma ya isa yace momy kar ki tsaya dawo da abin daya wuce kuma zagina fa tayi ai ko kina gurin kya ce na ladabtar da ita tace karya ne kace ta zage ka, kai dai kaje kaida Allah batun komawa kuma ba zata koma ba, yayi shiru yana tunanin yanda zaiyi shi dai yana son cika umarnin Haj shi ne yace momy kiyi hakuri dan Allah ba zan kuma ba jin haka sai tayi zaton aikin Malmin nasu ya cine,dama yace da kanshi zai zo yana bada hakuri kuma komai suka ce yayi musu zai yi masu,koda Haj Laure ta tuno da wannan kuma ta ga abinda ya faru(yana bada hakuri)sai tace mishi ko zata koma tana bukatar kudaden da zatayi gyaran daki,yace ba matsala zan bata tace to sai ka aiko da kudi in an gama gyaran gidan ta koma yace shi kenan zan zo anjima ko gobe na kawo,ya fita ranshi a bace ya tafi,yana mota Haj shi ta mishi waya wai ya dakko Mimin?yace sunce sai anyu mata gyaran daki ta ce sai ka bata ko nawa take so tunda ita yar rukon taka wa ya san kudin da ta samu a gurinka, yace ai nace zan bada tace to shi kenan,bayan ya kashe yayi tsaki gami da cewa an auran matsala

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Zaune nake cike fam tamkar zan fashe,yaynmu ya tafi tadi Aisha n Adams tai min waya sama sama muka yi hira saboda bana cikin hayyacina,na jefar da wayr kan kujera ina tsaki na dubi agogon bango awa uku kena da fitar shi lallai tadi yayi kyauzya shigo da sallama da kyar na amsa mishi ya zauna gami da fadin big gal bani abinci nace au bakaci a can ba?to nima ba zan baka ba ya tuno yanda suka rabu sai ya yi murmushi dan Allah big gal kar ki min haka ina jin yunwa kar na kara fusata nace ina da abinci amma ba zan baka ba kuma ka daina ce min big gal tunda yanxu ka daina sona,ya taso yana dariya yana fadin to ai yarinyar ma tace bata sona na mata tsufa,na dubeshi idona tam da hawaye nace kaine za'ace baa sonka bayan kana da kyau da kudi?ya jawoni jikinsa gaskene wai bata sona nace mata tazo taga biga gal a gidana nima na fasa,da na kula tsokanata yake sai naje na kawo miasi abinci.Rigima kala kala na dinga mishi yana lallashi gami da zolayata,ya basu kudi masu yawa amma har ynxu suna nan suna ja mishi rai a cewar su sai sun ja mishi aji gami da sashi ya sakeni yaje ya basu hakuri bisa tursasawar mahaifiyarsa nan suka rufe shi da masifa ita da uwarta bai tanka ba sai da suka gama sannan yace ni dai ina baku hakuri ne tazo mu tafi,Haj Laure tace sai ka je ka saki wannan matar taka! Ya mike da sauri Momi me kike fada?tace nace ka saki Iman, yayi mata duban kinyi kadan sannan yace Momy ki sake sabon tunani in har sai na saki Iman Mimi zata koma gidana to ta zauna dan ko mutuwa da ina da yanda zanyi da ba zan bari ta dauki Iman ba,zan iya rabuwa da kowa a ciki harda ku da dai na rabu da Iman, ya wuce fuuu!!yana fadin in ta ga dama ta dawo in kun ga dama kar ta dawo, yatafi ya kashe dukkan wayoyinshi dan ma kar a kirashi.Ina kishingide ina tunanin maganar Babana da ya ce inyi tunanin irin kasuwancin da zan fara a bani kudi, sai naji an rungumeni ta baya da sauri na tashi yaynmu ne yayi wata wawuyar ajiyar zuciya

nace guy Ify?yace sonki ne naji yana son ki ne naji yana son faso min zuciya ya fito waje, dadi ya kamani nace guy nima ina sonka ina tuna wata rana zaka iya min halin maza ka sakeni sai in ta kuka,yace big gal auran mu yafi auran zobe karfi ya shafi zoben hannuna tun wanda ya bani yace ki kalli cikin zoben nan me zaki gani na tsura masa ido(AA)nace AA ne a ciki yace to Amina Abdulrahman for ever zaki gani cikin zoben ta baya,kafin na kuma magana sai naji bakinshi cikin nawa ya mantar dani duniyar da muke.
Mimi ta kalli haj Laure tace gaky momy nifa zan koma gidan baban Dady tunda kin ga an samu wancan maganin yayi yazo duk abinda muka ce yayi ni kuma Iman in shiga ba sai in san yanda zanyi waje da ita baz Haj Laure tace shikenan tunda kin dage ai sai ki koma dan dama ni nufi na in karbar miki yanci,da sanyin safiya munyi lako lako ni da guy dina muna kari sai mukaji sallama tun kafin su gama shigowa muka gane su su Anty Mimi,ne nan da nan na ga yaynmu yayi kicin kicin da rai ya ajiye kofin hannunshi ya ja tsaki, nice na amsa musu sallamar su gami da gaishe su, basu amsa min ba sai suka nufi dakin Yayan mu ya yi dakin nima nayi nawa dakin.Sun danyi fushin su da juna na kwana biu suka shirya, sama sama take min magana nima bata gabana, kwata kwata kwananta uku yaynmu yayi shirin tfy, Haj shi taso ya tafi da Mimi sai yace shi ba zai tafi da kowa ba saboda wani club zasu siyeshi kuma bai san yanda abin zai kaya ba, tunda ya tafi ta tsiri yawo kullum ba ta nan,ni dama ban cika fitowa ba tunda abinci kowa nashi yake yi,yana kirana a waya musha hirar soyayya ya sanr dani wani club sun sayeshi miliyoyin kudi, kafin wata uku kowa ya san yaynmu yayi kudi gidan su ma ya sha gyara musamman dakin Hajrshi da dakin Alhj, motoci uku ya sai musu. Muma ya soma gina mana namu gidan a malali na gani na fada, tsarin gidan ma abin fda ne sai da ya turo da kudi kabiru yake gabatar da komai ,yanuwa da abokan arziki aiken kudi da tufafi kowa sai sa albarka yake.Ranar da zaizo bai fada ba zuwan bazata yayi,ni kadai ce a gidan Aunty Mimi an tafi yawon bin bokayen da aka saba, lokacin ko tunanin shi na keyi sai naji ana kwankwasa kofa cikin faduwar gaba na bude dan bansan kowane ne ba ina budewa

sai naga yaynmu ban san san da na daka tsalle na dane ahi ba shima cikin murna ya rungumeni muka shige cikin daki ya sauke ni akan kujera yace me ya same ki ne big gal?kinyi wani ciwo ne?naga kin rame? tunaninka guy shine ya ramar dani ya kuma rungume ni tare da yan wasanni yana gayamin yayi missn dina a lot,bai tambayeni Aunty Mimi ba,na shirya mishi abinci ina fadin ban san kana hanya ba guy dana shirya maka abinci na musamman amma gobe kace ma abokanka suzo lunchn ya ce to shi kenan big gal
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Da daddare na shirya mishi farar shinkafa da miyar dambun nama,yana ci na ajiye mishoi coke mai sanyi na gwangwani,ya dubeni tun yaushe Mimi ba ta nan?na ce dazu ta fita bai sake magana ba, muna tare har goma bata dawo ba na tsuke cikin riga da gajeren wando ,albarkatun kirjina duk sun fito,hakika kwalliyata ta firgita guy,dan na lura ya nuna kwalamar shi a fili,duk da fitar da Aunty Mimi tayi ta mugun bata mishi rai sai yace big gal zamuje dakina na ce guy dakinka fa kace me zanyi a ciki cikin zolaya nake magana yace lada zaki samo ko ba kya so? nace ina so mana amma sai dai ka goyani,ya ce abu mai sauki zo ki hau ya duka ni kuma na dane bayan shi muka fita muna dariya,mun kai tsakiyar falo sai ga Aunty Mimi ta shigo,ganinmu ya bata mamaki musamman ma da bata san yaynmu ya dawo ba,jakar hannunta ta fadi shi ko guy sai yayi tamkar bai ganta ba ya shige dakin shi,kan katifa muka fada ya nuna min karshen soyayya dama gashi tunda ya tafi ko yaushe cikin kitsa kaina na ke yar borno da yar arab suna kawo min kayan harka ga na Anty Yagana,Mama ma tana aiko min dana ta a gefe,rudewa yaynmu yayi ya gigita wane irin abu na bai min ba haka bayan nutsuwa tazo yace big gal dama kina bina bashi yau kam wannan rana nasa ta a cikin ranakun tarihi sannan duk wanda nake bi bashi ko nawa ne ranar yana tafe na dubeshi sai dariya nake yace au dariya ma na baki washe gari har tara na safe muna

manne da juna yaki i tashi wai sai nayi barci jiya banyi barci sosai ba,zan shiga da kaina in hada miki ke dai Allah yayi miki albarka me zakici?na dauka wasa ne ashe da gaske guy shine yayi mana break shi ya min wanka sannan nayi kwalliya muka fita sai gidanmu,can muka samu Aunty Mimi ina zaton kara ta kawo,kwana biu mun sha soyayya dan guy karshe ne ya iya tsantsar soyyaya, Aunty Mimi ta amshe shi suna tafke rigima sosai har yayi sanadin dukanta,bata dai tafi ba dan ya ce kuma in ta sake fita bai sani ba ta tafi kenan yace yana son ya tafi dani ne yana tunanin Hajiyarshi ,amma zai gwada yi mata maganar da na ga bai kuma maganar ba har tazo na san ba sa'a.bayan tafiyar shi na shiga laulayi kin gaya mishi nayi ko ya yi waya sai dai na daure mu sha hirarraki, ko asibiti naki yarda naje, nayi sa'a wannan karon ya dde sosai dan sunyi wasanni,ga na Nigeria da zasu yi na gasar cin kofin duniya,ni kaina ban san ko wata nawa bane amma har ya fito,Anty Mimi tunda taga cikin sai hankalinta ya tashi,suka shiga shige shige sai ga Aunty Mimi wai tana iya cin komai tayi ta lallashina naki karba ta rasa yanda zatayi dani kamar ta min dura can ta aje kwanon tace ina zuwa bari in aika direba ya kai dady gidan Haj..
Tana fita na aje mata kwanon a kofar daki na kulle kofata, ina kallonta ta window tana juya abincin tana magana ita kadai, tin da naga haka sai da nayi kwana uku ban fito ba,ina da komai na a kicin dina.Yau saturday;zaunenake ina kallon wasansu yaynmu na karshe, kuma wasane tun karfi ,suna wasa ne Brazil,ganin yanda Nigeria ke musu wasa ai suka shiga dukan su da wayo,kusa da raga wani dan Brazil ya sakarma yaynmu kafa a kirji, nan duka haushi ya kamani nace kai bari yaynmu ya dawo ni dai gara ya bar kwallo tunda duk abinda yake nema ya samu, sai kuma ya kama wata harkar tunda yana da kudi, duk da ture ture da kuma dukan da suke ma su yaynmu sai ga shi Allah ya basu sa'a sun lashe kofin,murna ba'a magana. Mutane suka yi ta bugo min waya suna min murna,Amira ma daga Yola sun kirani ita da mijinta,Babana ya kira yayi mana murna,bayan minti talatin na kirashi yace big gal kin kalli wasan mu ne? nace dole ne guy mun godewa Allah sai dai wanda ya

bige ka a kifjin nan ya bani haushi, yace ka da ki damu wasa ne.Patyn da aka shirya musu a Abuja nace zanzo sai yace kar nazo baya son ana kalle mishi ni,yaynmu akwai kishi.
Da kyar ya bari na bisu Mami zuwa yola gurin Amira,cikina sai girma yake ko su Mama basu san ina dashi ba, tunda sanda muka je Yola bai fito ba sai a bikin Saudatu suka ganshi, Anty Yagana kece min watan sa nawa ne?nace ban sani ba suka ce banje Asibiti bane nace sai yaynmu ya iso jibi bikin saudatun ma mama na ma waya kuma ta mishi waya.
Haj Yaya zaune a gaban boka tace gafarta malam so nake ka bani maganin da zamuyi amfani dashi yaron nan da yazo ya saki amaryarshi ya zauna da yar uwarshi,Boka yace ai Haj aikin gama ya gama dazu yar uwarki tazo ita da yarta sun amshi maganin da zasu kasheshi su zubar da cikin Amaryar su ci gado,Haj Yaya cikin tsoro tace kuma ka basu Malam?yace na basu ba aikin kudi bane kuma sun bani kudi sosai,Haj Yaya da tsoro da mamaki suka hanata magana can tace to ai malam ni ce mamarshi don dana ne shima, Bokan mamaki ya kamashi yace ai danki ne?tace dana ne wllh yace shine kike biye masu kuna mashi asiri lallai baki da hankali in ya mutu wanene da asara? Yarta zata auri wani kefa zaki haifi kamar shi?to aikin gama ya gama sai ki tashi in kinci sa'a basu bashi wani abinci ba ko abin sha, ki samu ki hana shi karasawa gidan ma don ko gidan ya taka sai yayi wani mummunan rashin Ify, maryar kuma in ta tsallaka kofar dakin cikin zai zube,ke kuma in kika amsa sallamar yar uwarki Haj Laure to zaki mutu, ai bata bari ya karasa ba ta tashi da gudu da gaggawa ta isa gida ta daga murya ta kira Kabir tana fadin Kabir kuna ina ynxu? Yace na dauko yaynmu ne yanzu mun isa gidanshi ta fasa ihu wayyo Kabir na shiga uku kada ku shiga gidan hannunta rike da wayan tana fadin kar ku shiga zai mutu idan kun shiga ko har kun shiga? yace eh,sai ko ta fadi sumammiya,Mama ta fito tana salati ruwa ta shafa mata, sauran kishiyoyin suna tsaye ta farko tana dubansu sai ta ganta a jikin Habiba nan ta soma kuka tana fadin ya mutu ko? Suka ce wa? tace yaynsu Haj Laure ta cuceni sannan ta fasa kuka mai karfi ,cikin kuka take masu bayani tana rufe baki sai akaga

yaynmu da Kabir don har sun kunna kai cikin gidan sukayi waya da Haj don haka a rude suka shigo tana ganinsu tace ka shiga gidan? yace a'a menene? nan tayi musu bayani, tsaki yaynmu ya ja yace ai gara in mutu in huta da wannan balain,Hajiyata kin bani mamaki ya juyo ta ruko shi ina zaka? wllh ba zaka wannan gida ba yace matata can tana cikin hatsari sai in tsaya,Mama ta dube shi kar kaje itama Allah zai kareta,yace haba mmn Sagir daina wannan magana,Haj Yaya tace Kabir jeka zo da Iman gashi ance kar ta tsallaka kofar dakinta,yaynmu yana min waya ina babban kicin ya ce kizo gida ynxu ko me kike kar ki koma daki na ce cikin tsoro Ify yaynmu? yace ba kalau ba,kar fa ki shiga daki!ki jira Kabir a waje zai zo.Sai da ana kwashe komai sannan na fita cikin tsoro kun sanni da rudewa,duk muna dakin Haj Yaya tana mana bayani cikin kuka ta soma rokon Mama gafara,Mama tace dama ban rike ki ba,ta dubeni yar nan kiyi hakuri nace ba komai Haj,kamar daga sama mukaji sallamar Haj Laure ba wanda ya amsa mata,kowa yayi shiru tace Murja! Murja!! Murja!!!
Sai ta sa ihu, kafin kace haka hauka tuburan,nan akayi waje da ita.can sai ga Aunty Mimi da Dady tana jina abinda ya faru sai kuka,yaynmu yace wa zakiyi ma kuka? Na sake ki tunda har kin amince ku kasheni sai a bar mana gida,Ummanki na gidanku sai kije kuyi jinya bani dana,ya amshi dady,
Ni da yaynmu duk muna gida bamu koma can gidanmu ba, Haj Yaya anyi nadama tunda ynxu dakinta nake kwana, ta hanani naje dakin Mama, yaynmu dadi kamar ya kasheshi.
Na fito wanka ina zaune a bakin gado ina shafa mai yaynmu ya shigo sai kallona yakeyi,yace Big gal yau fa zamu fita ina cikin takura fa masu aikin gidannan har ynxu ba su gama aikin ba duk kudin da nake turawa dan a takure nake,
Na harareshi ka kara hakuri guy ina jin kunyar su Haj Yaya da Mama,yace zan tambayar maki nace kaga ina da ciki ba zan iya maka komi ba yace ai hakan ma kinfi bani sha'awa bari haj ta shigo nace a'a guy ba ruwana.... muryar Haj ta hanani karasawa tace menene naji ana cewa bari inzo?ya sosa keya yace am..in...dama zamuje unguwa ne tace ina ce yace ba

nisa tayi murmushi kawai,mun fito na leka nace mama mun fita,ashe daki ya kama a Hamdala Hotel nan da nan sai gamu,lallai yaynmu yayi missing dina muna nan har tara nace mu tafi yace ina zuwa,ya fita can sai gashi da kaya niki niki ya dubeni yace duba kayane kala uku da takalma nace na menene yace siyowa nayi a waffa road don kwana uku na biya na zaro ido su mama fa da Haj? Yace karki damu ai sun san muna tare kuma tun da suka bani kesun san me zanyi ba gama cikina nan ba,nayi shiru kawai.munyi soyayya mai dadi cikin kwanakin bana zuwa ko ina gara shi in nace ina son wani abu ya kan fita nema min,ranar da mukaje gida kunya don kunya na kasa sukuni,yaynmu kam ko a jikinshi ba wanda yace ina muka je dama wayata ya kashe ta ma.
Wata na biu a gida 'lokacin yaynmu ma ya tafi ' aka gama gyaran gidanmu komai na cikin gidan babana ya zuba mana, Yaynmu yazo muka koma sabon gidan karshen haduwa ya hadu,kwananmu arbain na tashi da nakuda naso kada yaynmu ya tashi amma ina da ya kaini asibiti sam yaki fita daga dakin haihuwar duk in da nace wash nan sai ya rike mun da haihuwa tazo shi da likita suna rike dani gam na sukuto yar babyna mai kama da yaynmu tamkar kwabo da kwabo.
Gida aka maidani dakin Haj Yaya,naga gata ganin idona, ranar suna yarinya taci sunanta Murjanatu!sai muke ce mata Haj. Amira dasu Mami duk sunzo mana da danta Ammar, Amira da tsohon ciki.Bayan suna da sati daya yaynmu ya koma da niyar yin ritaya daga kwallo,Satinshi uku da tfy ya dawo,tsam ya rungumeni zamu kasance da juna big gal,ynxu wane abu zan fi mai da hankali a kai,nace kana da gurin sai da motoci kana da manyan stores sannan kana da gidan mai sai ka zaba.Haj ta shigo ganin muna rungume da juna tace yau naga ikon Allah kai kana da hankali? jego fa take yi ke kin zauna ya shigo maki da dan labubun jariri ta fita sai fada takeyi,nace ka gani guy na bani ya zanyi da kunya,yace dama zata koro mani ke da na huta da zaman kadaici,kai mata daya matsala ce dole na sake aure, nace dan Allah kar ka yi min haka guy yace to ba Haj tace kar ki shige min ba,nace ai a nan ne amma in mun koma gidanmu ai ka gane..na daga mishi gira yace naki wayon sai nayi amarya ya fita nace pls guy.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Kasuwanci,shago babana ya bude min kan titin maf road,kayan dubai nake saida wa yaynmu ne ke sa ana kawo min don yaki naje,shi kuma kasuwanci ya amsu ta ko ina,sannan ya fada harkar siyasa abin da ya karanta, mutane suka matsa sai ya fito takarar dan majalisar jiha, ni da ban amince ba sai da kyar,cikin sa'a ya cinye, lokacin Haj Baby nada shekara,Dady ya shigo mamy kizo papanmu yace kiyi sauri nace yana ina?dady yace yana dakinshi nace ina baby haj?yace tayi bacci a falo nace muje ku kwanta bayan mun kwantar dasu daki na koma na tsuke cikin riga karama ko cibi bata kai ba gabamta igiyoyin ne dama albarkatun gasu nan a fili sai gajeran wando ya dameni na gyara kaina na sa turaruka, yana bakin gado yana duba wasu takardu yana duba na yayi jifa da takardun kan durowa ya mike tsaye sai da nazo daf dashi sai kuma na daure fuska na juya da sauri yace menene big gal?nace cikin shagwaba ba kace sai kayi aure ba?yace wasa ne big gal ba zan iya aure ba ke kadai ce na juya na rungume shi yace yawwa big gal dina zaki kashe ni da soyayyya ya ja igiyar riga ta sai warware ta baya ya fada katifa nima na bishi.............Pens Uppp,cewar Auntyn mashi, Alhamdulillhi,Aunty Allah yakara Basira da Arziki, yakuma raya zuri'a,saikuma ni dana rubutamuke nakemuku fatan alkhairi,tsawon lokacin dana daukan kapin kammalashi nasan lallai na batawa wasu kamar yanda nasan nima wasu sunbatamin, saidai ta bangarena nayafemuku inna fatan kuma kuyafemin.
Jinjina gareku Admins namu,Allah yabar zumunci,Allah yakara hada kawunanmu. Sakon gaisuwa ga dunbin Masoya dake min magana, inna alfahari damu,sanna Dan Allah gamasu kallona abai bai Musamman yayin da sukamin magana ban amsaba Dan Allah kusani inna sane daku, wasu lokutan abin kefin karfina, nagode
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com

Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

DOCUMENT CREATED BY
ZAHARADEEN SHOMAR
WHATSAPP 08168575100